# Yadda Za Ka Yi Abota da Mutane Dabam-dabam

Wannan shafin rubutu zai taimaka maka (1) ka san ko su waye ne abokanka na kud-da-kud da kuma (2) ka gan yadda za ka iya yin abokantaka da mutane dabam-dabam.

**Abin da ya sa ya kamata ka ɗauki wannan matakin:** Idan kana yin abota da mutane iri ɗaya kawai, ba za ka sami damar sanin wasu mutanen kirki ba.

**1** A cikin wannan ƙaramin da'irar, ka rubuta sunayen abokanka na kud-da-kud.

**2** A cikin babban da'irar, ka rubuta sunayen mutanen da za ka so ka ƙara saninsu da kyau.




**Wata mai suna Melinda ta ce: "Yin abokantaka da waɗanda wani abu ya haɗa ka da su kawai zai hana ka samun abokan kirki tsakanin mutanen da suka fito daga wuri dabam da kai ko waɗanda ba tsaranka ba. Kari ga hakan, zai iya hana ka sanin yadda za ka zama mutumin kirki."**



www.jw.org/ha © 2017 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania

## Wane ne za ka iya kusanta don ka daɗa saninsa da kyau?

Ka zaɓi halaye uku da za ka so abokinka ya kasance da su. Idan za ka iya tuna wasu halayen da ba a rubuta a wannan jerin ba, ka rubuta su a cikin akwatunan da ba a rubuta kome ba.

✓

- Mai gaskiya
- Mutumin da ya san zafin kansa
- Mutumin da ba ya latti
- Mutumin da ba ya yin abu barkatai
- Mai fara'a
- Marar son kai
- Mai bayarwa
- Mai aiki da ƙwazo
- Mai kamun kai
- ....................................
- ....................................

Yanzu, ka rubuta sunayen mutanen da ka sani, da suke da waɗannan halayen. (*Ba sai lalle su tsaranka ba ne.*)

.............................................

.............................................

.............................................

.............................................



www.jw.org/ha © 2017 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania

# HAƊARI DA ALBARKA



Wane haɗari ne za ka jefa kanka a ciki idan ka kusaci wani da ba abokinka ba?

..............................................................................

..............................................................................

..............................................................................



Wane albarka ne za ka samu?

..............................................................................

..............................................................................

..............................................................................

## WACE SHAWARA CE ZA KA BA WASU?

Wata mai suna Emily ta ce: “Na lura cewa ina yawan magana da mutanen da suka riga suka zama abokaina ne. Ko da yake nakan ɗan yi magana da wasu, yawanci dai ina zuwa wurin waɗanda na san su ne. A ganina, abin da yake sa ni, ko kuma wasu matasa suke yin hakan shi ne, muna shakkar ko wasu za su so su yi abokantaka da mu. Hakan yana sa ba ma ƙoƙarin kusantar waɗanda ba mu san su ba.”

Wace shawara ce za ka ba Emily don ta daina jin tsoron kusantar mutanen da ba ta san su ba?

..............................................................................

..............................................................................

..............................................................................

..............................................................................



www.jw.org/ha © 2017 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania